# 2 Yohanna

1 Dattijon nan,

Zuwa ga uwargida zaɓaɓɓiya da kuma ’ya’yanta,
waɗanda nake ƙauna ƙwarai da gaske kuma ba ni kaɗai
ba, amma har da dukan waɗanda suka san gaskiya.
2 Muna ƙaunarku saboda gaskiyan nan, wadda take cik-
inmu za tă kuma kasance tare da mu har abada.

3 Alheri, jinƙai da kuma salama daga Allah Uba da kuma
Yesu Kiristi, Ɗan Uba, su kasance tare da mu cikin gaskiya
da ƙauna.

4 Na yi farin ciki ƙwarai, da na sami waɗansu ’ya’yanki
suna tafiya cikin gaskiya, kamar yadda Uba ya umarce mu.
5 Yanzu kuma, uwargida ƙaunatacciya, ba sabon umarni
nake rubuta miki ba sai dai wanda muke da shi tun farko.
Ina roƙo cewa mu ƙaunaci juna. 6 Ƙauna, ita ce mu yi
biyayya ga umarnansa. Kamar yadda kuka ji tun da fari,
umarninsa shi ne ku yi zaman ƙauna.

7 Masu ruɗi da yawa, waɗanda ba su yarda da zuwan
Yesu Kiristi cikin jiki ba, sun riga sun fito a duniya. Duk
irin mutumin nan mai ruɗi ne kuma magabcin Kiristi.
8 Ku lura don kada ku yi hasarar aikin da kuka yi, sai dai
ku sami cikakken lada. 9 Duk mutumin da bai tsaya a kan
koyarwar Kiristi ba, amma ya yi ƙari a kanta, mutumin
nan ba shi da Allah. Amma wanda ya tsaya a kan koyarwar
Kiristi, yana da Uban da kuma Ɗan. 10 Duk wanda ya zo
wurinku bai kuma kawo koyarwan nan ba, kada ku karɓe

shi a gidanku ko ku marabce shi. 11 Duk wanda ya karɓe
shi yana tarayya da mugun aikinsa ke nan.

12 Ina da abubuwa da dama da zan rubuta muku, sai dai ba na so in yi amfani da takarda da inki in rubuta. A maimako, ina fata in ziyarce ku in kuma yi magana da ku fuska da fuska, domin farin cikinmu yǎ zama cikakke.

13 'Ya'yan 'yar'uwarki wadda Allah ya keɓe, suna gaishe ku.

# Biblica® Buɗaɗɗen Littafi Mai Tsarki, Sabon Rai Don Kowa™

# Hausa: Biblica® Buɗaɗɗen Littafi Mai Tsarki, Sabon Rai Don Kowa™ (Bible) of Nigeria

copyright © 2020 Biblica, Inc.

Language: Hausa

Contributor: Biblica, Inc.

Biblica® Open Yoruba Contemporary Bible™
Copyright © 2009, 2017 by Biblica, Inc.
Used with permission. All rights reserved worldwide.
"Biblica" is a trademark registered in the United States Patent and Trademark Office by Biblica, Inc. Used with permission.
All content on open.bible is made available under a Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 License (http://creativecommons.org/licenses/by-sa/4.0/).
You are free to:

- Share — copy and redistribute the material in any medium or format
- Adapt — remix, transform, and build upon the material for any purpose, even commercially

Under the following conditions:

- Attribution — You must attribute the work as follows: "Original work available for free at www.biblica.com and open.bible" Attribution statements in derivative works should not in any way suggest that we endorse you or your use of this work.
- ShareAlike — If you remix, transform, or build upon the material, you must distribute your contributions under the same license as the original.

Use of trademarks: Biblica® is a trademark registered in the United States Patent and Trademark Office by Biblica, Inc. and may not be included on any derivative works. Unaltered content from open.bible must include the Biblica® trademark when distributed to others. If you alter the content in any way, you must remove the Biblica® trademark before distributing your work.
This translation is made available to you under the terms of the Creative Commons Attribution Share-Alike license 4.0.
You have permission to share and redistribute this Bible translation in any format and to make reasonable revisions and adaptations of this translation, provided that:

- You include the above copyright and source information.
- If you make any changes to the text, you must indicate that you did so in a way that makes it clear that the original licensor is not necessarily endorsing your changes.

If you redistribute this text, you must distribute your contributions under the same license as the original.

Pictures included with Scriptures and other documents on this site are licensed just for use with those Scriptures and documents. For other uses, please contact the respective copyright owners.

Note that in addition to the rules above, revising and adapting God's Word involves a great responsibility to be true to God's Word. See Revelation 22:18-19.

2021-11-15

---

PDF generated using Haiola and XeLaTeX on 29 Jan 2022 from source files dated 30 Dec 2021

18113be6-b3a0-530a-b78f-a25225282250